# Takardar Bayani

## Manyan nasihu guda 10 don gudanar da ziyarar lura da aiki

Yawancin ƙungiyoyi waɗanda ke sarrafawa da aiwatar da ayyuka za su buƙaci aiwatar da ayyukan sa ido da kimantawa a yayin tafiyar da aikin.

Wannan na iya zama:

- don bin diddigin ci gaba
- don auna tasiri ko nasarori
- dangane da bukatar mai bayarwa, ko damuwar da wata ma'aikaciya, mai sa kai, ko memba na al'umma suka lura da ita.

Saka ido ya haɗa da ayyukan nesa kamar karɓar rahotanni, bayanan ayyuka da rahotanni na kuɗi. Hakanan ana iya yin ziyarar fuska da fuska, wanda ya haɗa da tattaunawa, tattaunawar rukuni tare da membobin al'umma da mahalarta aikin, da kuma sharhi kan daftarin wurin aikin da duba wurare. An kirkiro wannan bayanin jagora ne don tallafawa ma'aikatan kungiyoyi wadanda ke shirin gudanar da ziyarar al'umma don lura da wani aikin da ake da shi don yin hakan cikin aminci da da'a.

### Abubuwan da za'a tuna

- ✓ Saka ido yakamata ya kasance fiye da biyayya ga mai bada gudumawa amma har ma da ilmantarwa da inganta ayyuka
- ✓ Kawai tattara abin da ake buƙata kuma mai amfani
- ✓ Abu mai muhimmanci ga ayyukan MEL shine kar a cutar da mutane
- ✓ Dole ne a aiwatar da nazarin hatsari kafin kowace ziyarar al'umma
- ✓ Duk wani bayani da aka yi yayin ziyarar dole ne a bayar da rahoto ta hanyoyin da aka amince da su
- ✓ Dole ne a gudanar da dukkan ayyukan ta hanyar lafiya da ɗa'a
- ✓ Ya kamata a nemi izinin duk ayyukan tattara bayanai, gami da tattaunawa ta yau da kullun tare da mahalarta aikin (masu cin gajiyarsa)
- ✓ Duk wani bayanin da aka tattara yayin ziyarar saka ido dole ne a adana shi lafiya kuma ayi amfani da shi da aminci

**Akwatin Ma'anoni:**

**Saka ido**: tsayayyen tsari da tattara bayanai na yau da kullun game da aiki akan lokaci.

**Ba da izinin**: na buƙatar bayar da isassun bayanai da suka dace game da bincike (ko ayyukan sa ido) don ba da damar masu amsawa su yi zaɓi mai ma'ana game da shiga ko a'a, da kuma tabbatar da babu wata tilastawa a bayyane ko a fakaice wacce za ta iya shafar shawararsu.

**Kada a cutar** : shine don kaucewa bayyanar da mutane ga ƙarin haɗari ta hanyar aikinmu. Yana buƙatar mu koma baya mu kalli muhallin da muke aiki don rage tasirin babbar illar da ayyukanmu ke da ita[1]. Wannan yana nuni ga masu bincike da masu tara bayanai da kuma masu amsawa da mahalarta.

[1] Dan Adamtaka da Haɗaka, 2018. Haɗawa da ka'idar 'Kada a cutari': Yadda za a ɗauki mataki ba tare da haifar da lahani ba. Tunani a kan bitar ayyukan ɗan Adam da Haɗaka.

## Shirya ziyarar

- ✓ Kasance an bayyana manufar ziyarar sa ido. Tabbatar da sanar da manufar ga ma'aikata na aikin da za ku ziyarta kafin zuwanku.
- ✓ Gano duk wani hatsari da ke iya tasowa sakamakon ziyarar aikin. Tsammaci kuma rage haɗari ta hanyar samar da ƙimar haɗarin don ziyararku.
  - Waɗanne rukunin mutane kuke so ku yi magana da su, shin akwai ɗayansu da ya fi sauƙin durkushewa, ko yara da matasa? Shin akwai wasu takamaiman haɗari a gare su?
  - Shin kuna da niyyar magance duk wasu batutuwa masu mahimmanci yayin ziyararku wanda zai iya ƙara kiyaye haɗarin mahalarta - gami da tashin hankali, zagi da tursasawa?
  - Shin akwai kungiyoyin al'umma da kuke magana da su wanda za su iya samun koma baya ko ramuwar gayya
    sakamakon shiga cikin aikin ko tattauna batutuwa da ku?
- ✓ Tabbatar da duk ma'aikatan da za su kawo ziyarar sun san ka'idojin aiki kuma sun sami horo kan kariya .
- ✓ Tabbatar kun san wanene ke shugabancin ayukan kariya kafin ziyararku.
- ✓ Tabbatar da kowa ya san yadda ake sanar da duk wani abin da ke iya faruwa wanda za a iya bayyanawa yayin ziyarar. Duk wani bayanin da aka gabatar yayin gudanar da ziyarar saka ido dole ne a bayar da rahoton ta hanyoyin da suka dace.
- ✓ Gano kungiyoyi daban-daban na masu ruwa da tsaki da kuke son haduwa da su da kuma irin tambayoyin da kuke son yi. Waɗannan na iya haɗawa da ma'aikata da masu ba da agaji, ƙungiyoyin ƙawance, ƙaramar hukuma, membobin al'umma da masu cin gajiyar kuma a tabbatar an sanar da su kafin ku ziyarce su.
- ✓ Duba cewa tambayoyinku ya zama dole. Shin akwai wasu hanyoyin tattara bayanai iri ɗaya?
- ✓ Idan ka shirya yin magana da yara ko matasa za ka iya buƙatar ƙarin kariya.
- ✓ Ya kamata a gano ayyukan tallafi na cikin gida kafin ziyarar idan har wasu matsalolin kariya suka taso yayin ganawa ko tattaunawa tare da mahalarta. Menene hanyar bayar da rahoto? Menene kuma ina hanyoyin tallafi na cikin gida don miƙawa gaba?

## Yayin ziyarar

- ✓ Ya kamata a karfafa matakai da tuntuba, ga dukan ma'aikata, masu sa kai da membobin al'umma. Duk wanda ke cikin aikin ya zama yana cikin ayyukan sa ido, kuma sakamakon dole ne ya zama mai amfani a gare su.
- ✓ Tabbatar cewa akwai tallafi ga kowane mai hallarta idan wani abu ya same su yayin ziyarar . Shin kun yi la'akari da buƙatu na musamman don yara ko mutanen da ke da nakasa?
- ✓ Tabbatar da yin tambayoyi masu mahimmanci a cikin kaɗaici tare da mai binciken da yake jinsi guda. Idan baza ku iya yin magana a ɓoye ba (wataƙila saboda COVID-19) la'akari da yin amfani da kalmomin shiga don tattauna batutuwa masu mahimmanci ko haskakawa idan suna cikin hatsari.
- ✓ Tabbatar cewa ƙungiyoyi da daidaikun da kuka gaiyyata za su iya/ko sami damar shiga wurin taron kuma ba a tsammanin su jira ba da dalili ba, ko tafiya a wasu lokutan da akwai matsala .
- ✓ Rukunoni masu jinsi daya, ya kamata mai irin jinsinsu ne zai jagorance su. Hakanan ya kamata masu binciken su zama masu jinsi guda..
- ✓ Tabbatar an sami izini don kowane shiga shirin, hotuna ko maganganu waɗanda aka tattara. Bayyana shigar su da yardarsu ta hanya mai sauki da fahimta, da kuma yadda za ayi amfani da bayanan. Shin kun bayyana cewa za su iya daina shiga a kowane lokaci? Idan kuna aiki tare da yara, tabbatar kun sami yarda daga iyaye ko mai kulawa.
- ✓ Tabbatar kun sanar da mahalarta yadda, da kuma wanda, za su iya kaiwa rahoton korafi ko damuwa game da aikin ko ziyarar sa ido lokacin da kuka tashi,kuma yaya za'a amsa shi.
- ✓ Tabbatar da godewa kowa don halarta da haɗin kai da aka bayar ga ziyararku.

## Kare bayanai da tsare sirri

- ✓ Tabbatar da tsare sirri, sirri da boye suna ta hanyar sakaya bayanan da aka tattara tare da cire duk wasu abubuwa da za a iya ganowa na abubuwan da suka faru ga mutum.
- ✓ Tabbatar cewa babu wani hatsari ga sirrin da tsarin adana bayanai da aka gabatar akan shafin. Ta yaya ake adana bayanai a wurin aikin? Shin kwafin rijistar takardun aikin, waɗanda za su iya haɗawa da sunaye aka adana a loka ko durowa? An adana kwafin dijital kuma an kiyaye kalmar sirri akan kwamfutocin aikin da kwamfyutocin dorawa a cinya?
- ✓ Yi la'akari da ko ya zama dole a lura da sunan mambobi yayin ziyarar sa ido - wannan da wuya ya zama dole. Ya kamata a kare yadda za a gane duk mahalarta.
- ✓ Kar a taba tambayar kowa ya bayyana wani bayani na sirri.

## Bayan ziyara

- ✓ Shirya taƙaitaccen bayanin ziyararku da tunaninku da kuma abubuwan da aka gano don rabawa ga wadanda kuka yi magana da su.
- ✓ Tabbatar cewa duk takardun bayanan tattaunawarku an adana su ko kuma a lalata su idan ba'a buƙatar su.
- ✓ Yi bitar kowane bayanin da aka tattara game da damuwa da kiyayewa da kuma bayar da rahoton duk wani yanki na damuwa zuwa wurin damuwa da kiyayewa. Shin kuna yin tambayoyi game da tashin hankali, cin zarafi ta fuskar jima'i, tursasawa ta fuskar jima'i,yin amfani da dama ko horon wuce ƙima?